# Littafi mai Tsarki na yara

## Ke gabatar da



# Ruth: Labarin Soyayya

**Wanda ya Rubuta: Edward Hughes**

**Mai Zane: Janie Forest**
**Alastair Paterson**

**Mai niyyan daukan nauyi: Lyn Doerksen**

**Fassarawa: Bible Society Nigeria**

**Wanda ya Wallafa: Bible for Children**
**www.M1914.org**

**©2024 Bible for Children, Inc.**
**Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan har ba zaku sayar da shi.**

**Bari a ce ka sadu da kakanin iyayenka, da iyayensu da duka mutanen da aka haifa kafin kai a iyalinka, za ka yi mamaki irin mutanen da dama suke. A cikin Littafi Mai Tsarki, daya daga cikin kakanin Yesu ita ce Rut – 'yar Mowab wadda da tana bautan gumaka.**



Labarin Rut ya fara ne a Isra'ila bayan lokacin Samson, lokacin da mutanen Allah sun bar yarda da yin biyayya ga Allah. Wani tsananin yunwa ya zo wa kasar. Ka san ko mene ne tsananin yunwa? Haka ne! Tsananin yunwa shi ne lokacin da babu 'ya'yan itace, ko hatsi yake tsira, sai dabbobi, wani lokaci har ma mutane suna mutuwa saboda yunwa.





**Wani mutum mai suna Elimelek, ya bar Baitalami tare da matansa da ‘ya’yansa biyu, domin neman abinci. Ya tafi Mowab, wani kasa inda mutane suke bauta wa gumaka.**



Abubuwa ba
su tafi daidai
kamar yadda Ebimelek da iyalinsa suke so
ba a Mowab.  Ya mutu, sai ‘ya’yansa biyu
su ma suka
mutu.




Matarsa Na’omi ce aka bari da matan
‘ya’yansa guda biyu, wato Rut da Orfa.
‘Yan matan duka su biyu ‘yan Mowab ne.

Na’omi, gwauruwa ce yanzu, ta ji labari cewa Ubangiji ya ziyarci mutanensa ya ba su abinci. Sai ta dauki ra’ayi za ta koma kasarta. To mene ne ‘yan mata biyun nan za su yi? Na’omi ta ba su shawara su zauna a Mowab su sake yin wani aure.



**Orfa ta koma zuwa wurin iyalinta. Amma Rut ta ki. Maimako, sai Rut ta yi wata waka mai kyau wadda ta yi alkawari cewa ba za ta rabu da surukinta ba.**





**Abokan Na’omi na da sun yi farin ciki cewa ta dawo gida a Baitalami. Amma ta ce su kira ta “Mara” (daci) maimakon Na’omi (dadi). “Gama Maidukka ya bi da ni cikin daci.” Na’omi ta dawo babu kome a hannu – sai dai Rut.**



Ko da yake Rut ta bauta wa gumaka kamar sauran mutane a Mowab, yanzu ta koma tana sujada ga Allah Mai Rai na Isra’ila.  Rut ta yi iyakacin kokarinta domin ta tabbatar Na’omi ta sami isashen abin da za ta ci.  Kowace rana tana bin masu girbin gonaki domin ta yi roron abin da aka bari a gonakin.







**Bowaz, mai gonar, ya ji labarin halin kirkin Rut game da surukar ta. Sa'ad da ya hadu da ita, Bowaz ya taimake ta ta wurin ba da umurni ga masu girbin sa su dan bar 'yan hatsi da gangan. Sai Bowaz ya fara son Rut.**



**Sa’ad da Rut ta gaya wa surukar ta game da halin kirki na Bowaz, sai tsohuwar ta yabe Allah. “Mutumin daga dangin mu ne, wani na kurkusa da zuriyarmu.”**





**Sa’ad da lokaci na wucewa, Bowaz ya fara so ya auri Rut sai ya lura da Na’omi da gonan iyalinta. Amma wani daga danginsu ya riga ya fara sa ido. Wannan mutumi yana son gonar amma ba ya so ya auri Rut. Doka kuma ta ce ba zai so daya ya bar daya ba.**

**A zamaninsu, mutane ba sa shan hannu da juna domin shirya abu. Bowaz ya cire takalminsa a idon jama’a sai ya ba wa daya mutumin. Shi kenan an shirya kome. Rut za ta zama matarsa. Yanzu, da ita da Na’omi su membobin iyalin Bowaz ne.**





**Bowaz da Rut sun ba wa dansu na fari suna Obed. Ya zama kaka na Dawuda babban Sarki  na Isra’ila.**

**Amma abu mafi ban mamaki, jaririn nan Obed shi ne kakan kakanin Ubangiji Yesu Kiristi.  Yesu ya fito daga iyalin Dawuda ne domin ya zama Sarkin Sarakuna da Mai Ceto na duniya.**



# Ruth: Labarin Soyayya

**Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki**

**a na samu a**

**Rut**

**“Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske.” Zabura 119:130**

# KARSHE

16

60

**Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.**

**Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.**

**Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:**
**Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.**

**Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16**